**Rariya**
February 10 ·
KISAN SHEIK JA'AFAR

Masu Yin Zargi Akan Rashin Dalili Ku Ji Tsoron Allah

Daga Datti Assalafiy

Na taba yin dogon rubutu kusan shekara uku yanzu tun bana tare da ra'ayin siyasar Malam Ibrahim Shekarau akan wadanda binciken mu na sirri ya tabbatar mana suke da hannu cikin kisan da aka yi wa Malam Ja'afar da Albaniy Zaria lokacin da aka ce wai an gano wata takarda a gidan Sanata Danjuma Goje wacce take dauke da jawabin yadda aka tsara kisan Malam Ja'afar, wallahi jama'a ku daina zargin kowa sai 'yan Boko Haram.

Allah ne masanin gaskiya, amma dai ni iya abinda binciken mu na sirri da tuntuba tun daga tushe ya tabbatar kuma ko a gaban Allah zan bada shaida akai shine 'yan Boko Haram ko ince wani bangaren 'yan Boko Haram wadanda sune asalin wadanda suka kafa kungiyar tun a shekarar 2002 wadanda aka fi sani da "Yan Kanamma" sune suka kashe Malam Ja'afar Mahmud Adam (Allah Ya karbi shahadarshi), su 'yan Boko Haram din da kansu sun tabbatar da hakan, duk da cewa suna da sabani kan cewa jinin Malam Ja'afar ya halatta ko bai halattaba? Amma Wallahi sune suka kashe shi.

Bayan sun kashe shi ne suka je suka yi tunga a FANSHEKARA suka yi ta kashe jami'an tsaro, har police Area Commander sun kashe, kafin da suka ga za'a cimma su sai suka sulale suka koma "SAHARA" Yankin ALGERIA da MALI, domin tun lokacin da aka tarwatsa su a garin Kanamma dake jihar Yobe inda aka kashe Shugabansu na farko wato Muhammad Ali ba a sake jin duriyar su ba.

To sauran wadanda suka tsere daga wannan fadan tsakaninsu da jami'an tsaro sai suka gudu suka bar Nijeriya suka koma Algeria inda suka hadu da Kungiyar Alqa'idah dake Magrib (AQMI) inda suka samo horo na yaki da hada bama-bamai, to su wadannan Mutanen sune suka dawo suka kashe Malam Ja'afar Mahmud Adam Kano (Rh).

Dalilin kisan sun ce Khawarij ne yaki basu goyon bayan a kaddamar da jihadi
Kuma awancan lokacin su 'Yan Kanamma karkashin jagorancin shugabansu Muhammad Ali basa tare da su Muhammad Yusuf na Boko Haram, a wani lokacin ma kafirtashi sukeyi, amma daga baya sun dawo Kasarnan suma suka hadu da Mutanen Muhammad Yusuf din, kuma bayan Muhammad Yusuf ya shelanta jihadin an kasheshi, su 'Yan Kanamma sune sukayi ta horar da 'Yan Boko Haram da koya musu yadda ake harbin bindiga da kuma yadda ake hada bama-bamai.

Cikin wadannan mutane 'Yan Kanamma da suka kashe Malam Ja'afar akwai IBRAHIM AL-MUHAJIR UQUBA yafi shahara da sunan ALHAJI FARI ga hotonsa nan na daura a wannan rubutun, shine ya jagoranci kisan Malam Ja'afar Kano, amma baya raye yanzu, dakarun sojin Nigeria sun samu nasaran kasheshi a garin Bama jihar Borno a shekarar 2014, su kansu sojojin basu san waye suka kashe ba a lokacin, don a wannan ranar itace ranar farko da Boko Haram suka kaddamar da hari a garin Bama karkashin jagorancin shi Uquba din (Alhaji Fari), suka fasa dakin ajiyar makamai na sojoji da aka ginashi a karkashin kasa bayan sojoji sun gudu suka kwashe makaman, to motar da zata kwashi makaman ta kai musu jeji tayi kadan, shine sai suka debi na diba akan zasuje su dawo su kwashe sauran makaman, sai Uqubah tare da wasu mutum hudu yace zai jirasu suje su dawo, bayan sun tafi; can kuma sojoji sunje sun kara karfi sun dawo sai suka tarar da Uqubah da yaransa, anan akayi musayen wuta, daya daga cikin tankokin yakin sojoji tabi ta kan Uqubah ta takashi ya mutu nan take

Bayan su kuma wadancan 'yan Boko Haram sun tafi kaiwa makaman jeji sai motar ma ta lalace a hanya, sai suka dawo da baya inda sukazo suka tarar da gawar Uqubah da na yaransa, sojoji kuma sun shiga cikin garin Bama sunja tunga, 'yan Boko Haram din a lokacin sai suka fusata zasu sake afkawa sojoji sai wani kwamandansu mai suna Kaka Allai yace a'ah a dauke gawar mamatansu a koma jeji, wannan shine karshen Uqubah wanda ya jagoranci kashe Malam Ja'afar, Amma har yanzu markazinsa (Uqubah) yana nan yamma da Farisu kusa da inda shekau ya taba boyewa a cikin jejin Sambisa.

Kuma wannan Uqubah din babban mabarnaci ne, ya kware a dukkan wani fanni na ta'addanci, su suka fara kowaya 'yan Boko Haram dukkan wani nau'i na ta'addanci, shine farkon wanda suka fara shiga jejin

Sambisa suka kafa sansani, lokacin farko farkon 'daukar makamin Boko Haram shi yake koyawa yara yadda ake hari a kashe mutum a cikin jeji sai su dawo cikin garin Maiduguri suna kashe mutane, akwai wansa uwa daya uba daya kafin aci amanata a shekarar 2017 nasan yana raye babban 'dan kasuwane a birnin Maiduguri

Lokacin da maciya amanar tsaron Nigeria kuma maciya amanar shugaba Buhari sukaci amanata suka kaini Abuja, gurin da aka boyeni a karkashin Kasa ( underground cell), na hadu da daya daga cikin yaran da Uqubah ya horar dasu ayyukan ta'addanci har tankokin yaki ya iya sarrafawa, amma ya bijirewa Shekau ya koma bangaren Al-barnawiy shima ya tabbatar min da cewa Uqubah ne ya jagoranci kisan Malam Ja'afar amma ba kowane zai sani ba hatta a cikin 'yan Boko Haram din sai masu matsayi

Su Mamman Nur Al-qadi daya daga cikin manyan daliban Muhammad Yusuf akwai lokacin da yace basu da hanu wajen kisan Shaikh Ja'afar, kai da farko ma har suna yiwa 'yan uwansu 'yan Kanamma inkari cewa basu kyauta ba da suka kashe Sheikh Ja'afar, kuma shiyasa su Mamman Nur har sukaje ta'aziyyan rasuwan Malam Ja'afar din a Kano, idan makusantan Malam Ja'afar da suka karbi ta'aziyyar rasuwarsa sun karanta wannan rubutun zasu tuna lokacin da su Mamman Nur suka kawo ta'aziyya a shekarar 2007 kenan kafin suma su shelanta jihadi

Amma kuma daga baya su Mamman Nur sun ce kashe Malam Ja'afar da 'yan uwansu 'yan Kanamma suka yi dai-dai ne, domin wai Malam Ja'afar kafiri ne khawarin Malamin gwamnati, dan haka jininsa ya halatta tunda yana matsayin malaminsu a lokacin amma ya ki goya musu baya a dauki makami a kaddamar da jihadi.

Daga cikin abinda zai tabbatar da cewa 'Yan boko haram ne suka kasheshi, bayan sun kasheshi ai sunci gaba da kashe Malaman Ahlussunnah, misali a cikin garin Maiduguri kadai inba Allah ba babu wanda yasan adadin Malaman da suka kashe, misali Malam Ibrahim Gomari, Malam Bashir kacalla da sauransu.

Kuma kisan Shaikh Albany Zaria ya dada bayyanawa al'umma karara cewa su suka kashe Malam Ja'afar Mahmud Adam ( rahimahullah ) domin idan aka dubi salon da sukabi suka kashe su duk yana kama da juna.

Wasu suna cewa ai Malam Albaniy Zaria yayi lecture mai taken WA YA KASHE MALAM JA'AFAR kuma ya zargi Malam Ibrahim Shekarau, jama'a ina tabbatar muku da cewa kafin Boko Haram su kashe Malam Albaniy Zaria sai da ya dawo ya fahimci cewa Boko Haram ne suka kashe Malam Ja'afar Kano, kuma ya fadi hakan a wasu karatunshi.

Sa'annan inda ace masu zargin Malam Ibrahim Shekarau sun saurari karatun Muhammad Yusuf da yayi lokacin da wasu mabiyyansa su kace ai bai kamata su kafirta dukkan al'umma ba, domin akwai "Al-uzuru bil-jahal", a cikin fatawar da Muhammad Yusuf ya basu ya bayyana karara yace su idan suka tada yaki to da "Yan izala" zasu fara musamman Malamansu.., don haka jama'a ku dena zargin Malam Ibrahim Shekarau da hanu cikin kisan da akayiwa Malam Ja'afar, ku dune daukan alhakkinsa.

Allah Ka jikan Malam Ja'afar Ka sa ya dace da mutuwar shahada. Amin.

See Translation

Rariya
@rariyajarida

- Home
- About
- Photos
- Reviews
- Videos
- Twitter
- YouTube
- Google+
- **Posts**
- Community
- Info and Ads

Create a Page

Like · Follow · Share · ...

**Rariya**
February 10 ·

KISAN SHEIK JA'AFAR

Masu Yin Zargi Akan Rashin Dalili Ku Ji Tsoron Allah

Daga Datti Assalafiy

Na taba yin dogon rubutu kusan shekara uku yanzu tun bana tare da ra'ayin siyasar Malam Ibrahim Shekarau akan wadanda binciken mu na sirri ya tabbatar mana suke da hannu cikin kisan da aka yi wa Malam Ja'afar da Albaniy Zaria lokacin da aka ce wai an gano wata takarda a gidan Sanata Danjuma Goje wacce take dauke da jawabin yadda aka tsara kisan Malam Ja'afar, wallahi jama'a ku daina zargin kowa sai 'yan Boko Haram.

Allah ne masanin gaskiya, amma dai ni iya abinda binciken mu na sirri da tuntuba tun daga tushe ya tabbatar kuma ko a gaban Allah zan bada shaida akai shine 'yan Boko Haram ko ince wani bangaren 'yan Boko Haram wadanda sune asalin wadanda suka kafa kungiyar tun a shekarar 2002 wadanda aka fi sani da "Yan Kanamma" sune suka kashe Malam Ja'afar Mahmud Adam (Allah Ya karbi shahadarshi), su 'yan Boko Haram din da kansu sun tabbatar da hakan, duk da cewa suna da sabani kan cewa jinin Malam Ja'afar ya halatta ko bai halattaba? Amma Wallahi sune suka kashe shi.

Bayan sun kashe shi ne suka je suka yi tunga a FANSHEKARA suka yi ta kashe jami'an tsaro, har police Area Commander sun kashe, kafin da suka ga za'a cimma su sai suka sulale suka koma "SAHARA" Yankin

438438
142 Comments60 Shares


APC



**Datti Assalafiy**

April 15 at 2:21 PM ·

WATA SABUWAR MASIFA MAI KAMA DA ANNOBAR " 'YAN KANAMMA" DA TAKE TUNKARAR MANYAN MALAMAN ADDININ MUSULUNCI A NIGERIA

Akwai wasu tsirarun Malamai da dalibansu marassa kunya babu abinda suka shagala dashi a wannan lokacin face kokarin alakanta wasu manyan Malaman addinin Musulunci da akidar khawarijanci, wato 'yan ta'adda, wannan masifa ne jama'a, domin da haka 'yan Kanamma wato 'yan Boko Haram na farko da sukayi sansani a Fanshekara karkashin jagorancin Muhammad Ali wanda aka hallakashi tun a wancan lokaci da suka kashe wani Area Commander na 'yan sanda suka fara jifan Malaman da basa kan fahintarsu da kalmar khawarij

Bayan haduwar Muhammad Yusuf na Boko Haram da Muhammad Ali na 'Yan Kanamma sai suka fara'a da'awar jifan manyan Malaman addinin Musulunci a Nigeria irin su Malam Ja'afar da kalmomin Khawarij suna fitar dasu daga da'irar Sunnah, karshe suka halasta jinin Malam Ja'afar kuma suka kashe shi, to yanzu ma akwai wasu sun taso suna jifan manyan Malamanmu da kalmar khawarij, kuma idan ba'a manta ba Muhammad Yusuf yasha nanata cewa idan suka dauki Makami da Malaman addinin Musulunci zasu fara, kuma hakan sukayi

Kafin na bada shawara ga Malaman da ake jifansu da kalmar khawarij ga wani takaitaccen bayani da Ash-sheikh Dr. Aliyu Muh'd Sani (H) yayi akan asalin ma'anar Khawarij:
!
Ni fa na gamsu cewa; masu danganta Dr. Mansur Sokoto da Dr. Bashir Aliyu Kano ga Khawarijawa sun jahilci hakikanin Khawarijawa.

Ai su Khawarijawa Annabi (saw) ne ya bayyana siffofinsu a fili, daga ciki ya nuna:
1- Sun fi kowa Sallah da Azumi da karatun Alkur'ani, amma maras amfani.
2- Suna "Muruqi" wato suna fita daga Addini.
3- Shi ya sa suke kafirta al'ummar Musulmi gaba daya.
4- Suna kashe Musulmai su bar Kafirai.

Saboda haka ne Annabi (saw) ya zarge su zargi mai tsanani, har ya kwadaitar a kan yakarsu da kashe su (khawarij)

To in ka ce: Dr. Mansur Sokoto da Dr. Bashir Aliyu Kano ko wani daga cikin Malamai Ahlus Sunna yana kan tafarkin Khawarijawa to fa kana nufin suna da wadancan siffofi da Annabi (saw) ya yi bayani. Don haka hukuncinsu shi ne a yake su a kashe su.

To abin tambaya a nan; yaushe su Dr. Mansur Sokoto suka siffantu da wadancan siffofi har da za a danganta su da Khawarijawa?!

Saboda haka da wannan za ka san cewa; duk wanda ya jingina su Dr. Mansur Sokoto ga Khawarijawa to bai fahimci su waye Khawarijawa ba, ko kuma kawai zaluntarsu yake son yi.

Ni kuma shawaran da nakeso na baiwa wadannan manyan malamai namu da ake jifansu da kalmar khawarij shine kuyi kokari ku inganta

tsaron kanku, sannan ku fara tunanin daukar mataki na shari'a saboda wannan kalma da ake jifanku da ita bata da maraba da yiwa rayuwarku barazana, don haka ku gaggauta daukar matakin shari'ah zuwa ga hukumomin tsaro mafi kusa da ku

Allah Ka tsare mana Malamanmu daga dukkan sharri da batanci da cutarwa Amin

See Translation





538 210 Comments 95 Shares

Like Comment Share



**Datti Assalafiy**
April 13 at 10:08 PM ·

SHAHADAR KHADIMUL QUR'AN

Yau shekaru 12 cif da 'yan Boko Haram suka zubar da jini mafi tsada a Nigeria jinin Sheikh Ja'afar Mahmud Adam Kano, wanda muke kyautata masa zaton ya dace da mutuwar shahada insha Allah

Shahararren kwamandan kungiyar Boko Haram Ibrahim Al-muhajir Uqubah wanda yafi shahara da sunan Alhaji Fari shine ya jagoranci kisan gillar da suka yiwa Malam Ja'afar


Sai dai wani labari mai dadi jama'a; Alhaji Fari ya jagoranci kisan Malam Ja'afar da bindiga kirar AK47 sukayi ajalinsa, shi kuma Alhaji Fari tankar yakin sojojin Nigeria ita tayi ajalinsa, takashi tayi ta markade tsinanne a garin Bama jihar Borno a shekarar 2014 ranar da ya jagoranci 'yan uwansa 'yan ta'adda sukayi hari suka fasa dakin ajiyar makaman sojoji na karkashin kasa

Tsakanin wanda harsashin bindiga kirar AK47 tayi ajalinsa da wanda tankar yakin sojoji tayi ajalinsa ta takashi aka markade buzun gawansa a kasa wannene yafi yin mutuwar wulakanci jama'a?

Karshen rayuwar kenan, Alhaji Fari ya tafi gurin da Malam Ja'afar yaje, sai ranar Hisabi Malam Ja'afar zai tashi jinin jikinsa yana zuba yana fitar da kamshin turaren Almiski, ya shako wuyan Alhaji Fari zuwa gaban Allah yace Allah gashi nan ka tambayeshi laifin me nayi ya zubar da jini na?

Allah Ka kyautata makwancin Malam Ja'afar da na aboki amininshi Malam Albaniy Zaria
Allah Ka karbi shahadarsu Ka hada fuskokinmu da nasu a cikin Aljannah Madaukakiya Amin

See Translation






845 · 408 Comments · 134 Shares